Lallai Allah - Mai girma da ɗaukaka - ba Ya bacci, kuma ba ya kamata gareShi Ya yi bacci

Daga Abu Musa - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya tsaya a cikinmu da wasu kalmomi biyar, sai ya ce: «Lallai Allah - Mai girma da ɗaukaka - ba Ya bacci, kuma ba ya kamata gareShi Ya yi bacci, Yana ƙasa da ma'auni kuma Yana ɗaga shi, ana ɗaga aikin dare kafin aikin rana zuwa gare Shi, da aikin rana kafin aikin dare, shamakinSa shi ne haske, da ace zai yaye shi da hasken fuskarSa ya ƙona inda ganinsa ya tiƙe daga halittarSa».

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya tsaya yana mai huɗuba a cikin sahabbansa da wasu jumloli biyar cikakku, su ne: Na farko: Allah - Mai girma da ɗaukaka - ba Ya bacci. Na biyu: Bacci ya koru a cikin haƙƙinSa; saboda cikar ƘayyumiyyarSa da kuma rayuwarSa. Na uku: Allah Yana ƙasa da ma'auni kuma Yana ɗaga shi da abin da ake auna ayyukan bayin da aka ɗaukakasu masu hawa zuwa gareShi, kuma ana aunawa daga arziƙansu masu sauka zuwa ƙasa, arziƙin da shine rabon kowanne abin halitta tsarki ya tabbatar maSa Yana ƙasƙantar da shi sai Ya ƙanƙanta shi, kuma Yana ɗaukaka shi sai Ya yalwata shi. Na huɗu: Ana ɗaga abin da bayi suka aikata da daddare kafin yinin da zai zo a bayansa, da kuma aikinsu da rana kafin daren dake bayansa; Mala'iku masu kiyaye ayyuka suna hawa sama da ayyukan dare bayan ƙarewarsa a farkon yini, kuma suna hawa da ayyukan rana bayan ƙarewarsa a cikin farkon dare. Na biyar: HijabinSa mai hana ganinSa shi ne cikakken haske ko wuta, da zai yaye shi da hasken fuskarSa ya ƙona inda ganinSa ya tiƙe a halittarSa; hasken fuskarSa shi ne haskenSa da kuma ɗaukakarSa da kwarjininSa. Abin ƙaddarawa: Da a ce Ya gusar Ya yaye abin da ke hana ganinSa shine hijabi, Ya yi tajalli ga halittarSa da hasken fuskarSa sun ƙona inda ganinSa ya tiƙe daga halittarSa; sune dukkanin halittu; domin cewa ganinSa - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka - mai kewaye sani ne da dukkanin kasantattu.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/65114